JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA 25 Jimada al- Ah-khir, 1443
MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI 28 Junairu, 2022

(1)

# HAƘƘOƘIN ƘASA DA SADAUKAR DA KAI WAJEN BA TA KARIYA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Ku yi riƙo da igiyar Allah kada ku soma ku rarraba)** [Ali Imran: 103], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai ƙasa tana da babban matsayi a zukatan 'ya'yanta, kishin ƙasa fiɗira ce wadda Allah ya halicci zukatan bil'adama akanta, al- Asma'iy (Allah ya ƙara masa rahama) yana cewa: **Idan kana son ka gane halaccin mutum, da cika alƙawarinsa, ka duba irin yanda yake begen ƙasarsa, da yanda yake son 'yan uwansa, da kuma irin yanda yake tunawa da tarihinsa da ya wuce.**.

Lallai son ƙasa, da nuna kishinta abu ne da ya wajaba a addinance; saboda haka ne ma Shari'ar Musulunci take cike da kira zuwa ga ƙarfafa son ƙasa, da yin aiki tuƙuru wajen cigabanta, ga Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) nan lokacin da ya yi hijira zuwa garin Madina, ya kalli ƙasarsa Makka yana ban kwana da ita, yana cewa: **(Wane gari ne ya kai ki daɗi! Wane gari ne na fi so sama da ke?! Ba domin mutane na sun fitar da ni daga cikin ki ba da ban fita ba)**, haka ma lokacin da ya yi hijira ya zauna a garin Madina ya roƙi Allah Mai girma da ɗaukaka ya sanya masa soyayyar wannan gari, (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Ya Allah Ubangiji ka sanya mana soyayyar**

**garin Madina kaman yanda muke son garin Makka, ko sama da haka).**

Son ƙasa ba kalmomi ne da ake rerawa, ko wani take da ake furtawa ba; a'a, tsari ne na rayuwa, da sadaukar da kai, da ma sadaukar da dukan abubuwan da aka mallaka, zama ɗan ƙasa na haƙiƙa yana nufin kishin ƙasa, da kuma kiyaye tsaro da zaman lafiya da kwanciyar hankalinta, da kuma cigaba da ɗaukakanta, haka kuma da kiyaye haƙƙoƙi, da wajibai da suke da jiɓi da ita, shi kishin ƙasa na ainihi sadaukar da kai ne, da kuma yin tinƙaho da ƙasa, saboda lallai ƙasa ta cancanci mu sadaukar da kawunanmu saboda cigabanta da ba ta kariya..

A cikin muhimman haƙƙoƙin ƙasa da suke a kawunanmu akwai sadaukar da kai saboda da ita, babu shakka sadaukar da rayuwa shi ne yake akan ƙololuwar dukan nau'o'in sadaukar da kai, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(A cikin waɗannan mutanen da suka yi imani da Allah akwai gwarazan da suka yi wa Allah alƙawari jajircewa wajen yin yaƙi a tawagar Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), suka kuma cika wannan alƙawari da suka ɗauka, a cikinsu akwai waɗanda suka sami shahada, haka ma akwai waɗanda suke a raye suna tsumayar samun wannan muƙamin, ba su sauya wannan alƙawari da suka ɗauka da kansu ba, ba kuma su rage masa ƙarfi ba)** [al- Ahzab: 23], Lallai Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya yi wa waɗanda suke bai wa ƙasa kariya albishir, waɗanda suke sadaukar da rayuwar su saboda ita, ya yi masu albishir da samun tsira ga barin wuta, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Idanuwa guda biyu wuta ba za ta shafe su ba: idon da ya yi kuka saboda tsoron Allah, da idon da ya kwana yana tsaro saboda Allah)**, saboda

haka ne masu sadaukar da kawunansu suka zama zaɓi ne na Allah Maɗaukakin Sarki da yake yi a cikin muminai, suna kuma tare da Annabawa, da siddiƙai, da salihan bayin Allah, Allah mai girma yana cewa: **(Saboda kuma Allah ya bayyana waɗanda suka yi imani, ya kuma zaɓi Shahidai daga cikinku..)** [Ali Imran: 140], haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Duka waɗanda suke yi wa Allah da Manzon Allah biyayya, to lallai su ne suke cikin waɗanda Allah ya yi masu ni'imomi cikin Annabawa, da siddiƙai, da Shahidai, da salihan bayin Allah, kai lallai wannan abota ce da ta yi kyau matuƙa)** [an- Nisa'i: 69].

****

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, shugabanmu Annabi Muhammadu da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai a cikin haƙƙoƙin da ƙasa take da su akan 'ya'yanta akwai: fitowarsu ƙwansu da ƙwarkwatarsu domin bai wa ƙasar kariya, idan har buƙatar hakan ya taso, tun da kuwa sadaukar da rayuwarsu da bayar da jininsu a fagen kare ƙasa wajibi ne, to kuwa shiga cikin ayyukan da suka shafi cigaban ƙasa, da samun ɗaukakanta zai zama cikin sahun mafi raunin imani kenan, bai wuce babin nan na son ƙasa da nuna kishinta a aikace ba..

Ba wai mutanen da suke a yanzu ne kawai suke ɗaukan wahalhalu, da ɗawainiyar cigaban ƙasa ba, kuma hakan ba wai yana kan wasu banda wasu ba ne, hasali ma aiki ne na tare da dukan al'umma da suka wuce, da waɗanda suke a raye, da masu zuwa suke yi.

A cikin muhimman haƙƙoƙin ƙasa akwai: Jajircewa wajen gudanar da aiki, da kuma kyautata shi, Annabinmu (SallalLahu

alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah yana son idan wani daga cikinku zai yi aiki, ya kyautata wannan aikin).**

Haka ma akwai: Gabatar da duk abubuwan da tsarin aiki ya wajabta akan ma'aikata, shi aikin gwamnati amana ne, kuma alhaki ne da Shari'a ta wajabta, kishin ƙasa kuma ya tabbatar, saboda haka, yi wa aikin gwamnati riƙon sakainar kashi nau'i ne mai muni cikin nau'o'in ɓarna, da cin hanci da rashawa, saboda haka ya kamata mutum ya sanya zuciyarsa ta zama a raye a koda yaushe, kuma a farke, yana mai hararo maganar Allah mai girma da ɗaukaka da take cewa: **(Shi Allah yana tare da ku a duk lokacin na kuke, lallai Allah yana da cikakkiyar masaniya da abubuwan da kuke aikatawa)** [al- Hadid: 4].

Haka ma akwai: Girmama tutar ƙasa, da takenta, da duk wani abu da yake nuni zuwa gare ta, ita tuta alama ce ta ƙasa da dukan 'yan ƙasa a ciki da waje suke haɗu akanta, a ƙarƙashin inuwarta ne suke gabatar da dukan ayyukan da suke gabatarwa, saboda haka girmama ta ɗaya ne daga cikin muhimman ginshiƙai na gina ƙasa..

Haka ma akwai: Kyautata wakiltar ƙasa a ciki da wajenta, da ma duka wararen tarurruka na cikin ƙasa, da na waje, da kuma yi aiki wajen samun ɗaukakanta akan dukan ƙasashe, kowa ya yi iya abin da zai iya wajen zama jakadan alhairi ga ƙasarsa a duk inda yake.

Haka ma akwai: Rashin bayar da kowace irin dama da za a gegi ƙasar, ko a ci mutuncinta, ta hanyar magana, ko ta hanyar aiki, da kuma ƙalubalantar maƙiya ƙasa da dukan abubuwan da muke mallaka a duk sanda buƙatar hakan ya taso.

Ya Allah Ubangiji ka bai wa ƙasarmu kariya da sauran ƙasashen duniya baki ɗaya..